Mafi cancantar sharuɗɗa da za ku cika; su ne wadanda aka halatta muku mata da su

Daga Uƙubah Ibnu Amir - Allah Ya yarda da shi - ya ce: Manzon Allah - tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi - ya ce: Mafi cancantar sharuɗɗa da za ku cika; su ne wadanda aka halatta muku mata da su.
[Ingantacce ne] [Bukhari da Muslim ne suka rawaito shi]

Annabi tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi yana bayyana cewa mafi cancantar sharaɗin da za a cika shi ne wanda ya kasance dalili na halatta jin daɗi da mace, su ne sharuɗɗan da suke na halal ga mace ta nema a lokacin ɗaurin aure.

http://www.sunnah.global/hadeeth/ha/show/6021